


Hikimar Dila

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Hikimar Dila
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN


Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009




A Habasha an yi wani gandun dabbobi.
A cikin gandun akwai dabbobi iri-iri.
A gandun suna da tsarin zaɓen shugaba.
A kowace shekara sukan yi zaɓen shugaban.

Aikin shugaban shi ne kare su daga hari.
Harin ko na mutane ko na wasu dabbobi.
Da kiyaye filin kiwo da na shan ruwa.
Shugaban shi ke daidaita tsakaninsu.
Dole ya kasance mai basira da hazaka.
























Shekarar zaɓen shugaba ta zagayo.
Masu neman shugabanci sun fara fitowa.
Giwa na son shugabanci.
Zaki na son shugabanci.
Dila ma na son shugabanci.

Giwa tana ganin ita ta cancanta.
Zaki ma yana ganin ya cancanta.
Dila yana ganin ya fi cancanta.
Kowannensu yana da magoya baya.












Giwa ta na takama da girma jiki.
Zaki ya na takama da ƙarfin shi.
Dila ya na takama da hikimarsa.



Ranar zaɓen shugaban gandu ta zo.
Masu takara da magoya bayansu sun taru.
Kowa yana ganin shi ne ya fi cancanta.
Giwa na iƙirarin kare su daga hari.
Zaki na alfaharin kare filin kiwo.
Dila na fankama da hikimarsa.


Rigima ta taso tsakanin magoya bayansu.
Kowa ya ce na shi zai yi shugabanci.
An kasa fahimtar juna a tsakaninsu.
An ɓata lokaci ba a yi zaɓen ba.
Kowa ya kasa yiwa juna haƙuri.
An rasa mafita saboda hakan.






Ana hakan sai kurege ya zo da shawara.
Ya ce a kawo kunu mai zafi.
Don masu takara su sha.
Ta hakan za a gane wanda ya cancanta.
Kowa yana mamakin wannan shawarar.


An kawo kunu mai zafi.
Giwa ta kurɓi kunu.
Giwa ta zubar don zafi.
Aka ce zaki ya sha kunun.
Zaki ya cika bakinsa da kunun.
Zaki shi ma ya zubar don zafi.
An kawo kan dila.











Dila ya ce a ajiye kunun a rana.


Domin zafin rana ya ƙara wa kunun zafi.

Kowa yana mamakin bajintar dila.


Kunu ya sha rana.

Dila ya shanye kunu duka.

Shugabanci ba girman jiki ba ne.
Shugabanci ba ƙarfi ba ne.
Shugabanci hikima ne da basira.
Kowa ya fahimci juna.
An naɗa dila shugaba.
Dabbobi sun koma gida da murna.
Gandu ya zauna lafiya.







ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK